Na tambayi Abdullahi Bin Amr game da mafi tsananin abunda Mushirikai ga Manzon Allah SAW sai ya ce: Naga Uqubuta Bin Abi Muaix Manzon Allah SAW kuma yana Sallah, sai ya sanya Mayafinsa a wuyansa sai ya shaqeshi shaqa mai tsanani

Daga urwa Bn Zubair ya ce: "Na tambayi Abdullahi Bin Amr game da mafi tsananin abunda Mushirikai ga Manzon Allah SAW sai ya ce: Naga Uqubuta Bin Abi Muaix Manzon Allah SAW kuma yana Sallah, sai ya sanya Mayafinsa a wuyansa sai ya shaqeshi shaqa mai tsanani, sai Abubakar ya zo har ya ture shi, sai ya ce: "Yanzu zaku kashe Mutum don yace Allah ne Ubangijinsa, kuma bayan ya zo muku da Ayoyi Mabayyana daga Ubangijinku" { Ghafir: 28)

[Ingantacce ne] [Buhari ne ya rawaito shi]

Urwa Bn Zubair ya ce: "Na tambayi Abdullahi Bin Amr game da mafi tsananin abunda Mushirikai ga Manzon Allah SAW sai ya ce: Naga Uqubuta Bin Abi Muaix Manzon Allah SAW kuma yana Sallah, sai ya sanya Mayafinsa a wuyansa sai ya shaqeshi shaqa mai tsanani, sai Abubakar ya zo har ya ture shi, sai ya ce: "Yanzu zaku kashe Mutum don yace Allah ne Ubangijinsa, kuma bayan ya zo muku da Ayoyi Mabayyana daga Ubangijinku" {Ghafir: 28) wannan ita ce shaidar mafi munin Abunda Abdullahi ya gani -Allah ya yarda da shi- kuma Urwa ya tsaya kan wannan shi ne ma tsananin abunda ya gani tunda Urwa ya bada labarin cewa Nana Aisha -Allah ya yarda da ita ta bashi labarin sa cewa ta ce da Manzon Allah SAW shi ka tava samun wata rana mafi tsanani a gareka kamar ranar Uhud? sai ya ce: "Na gamu abunda na gamu da shi daga Mutanenki kuma mafi tsananinsu ya kasance a ranar Aqaba lokacin da na gabatar da kaina ga Ibn Abd ya lail Bn Abd Kulal, bai amsa mun ba abunda na so, sai na tafi ina cikin vacin rai a fuskata, ban farka ba sai ina Qarn tha'alib sai na xaga kaina, sai ga girgije ya lulluveni, sai na duba sai Jibril a cikinsa, sai ya irani sai ya ce Allah yaji Maganar Mutanenka gareka, kuma da abunda suka mayar maka, haqiqa ya aiko Maka Mala'ika Duwatsu ka umarceshi da abunda ka so akan su, sai Mala'ikan Duwatsu ya kirani yayi mun Sallam sannan ya ce: ya Muhammad sai ya ce: Wancan sai abunda kaso in kaso in jeho shi akansu ? sai Manzon Allah SAW ya ce: aa ina son son a samu waxanda zasu futo daga ysatsonsu wanda zai bautawa shi kaxai, baya masa Shirka da komai" Buhari da Muslim suka rawaito shi